gudanar da aikin kuma za a baka rasidin shaidar biyan kudin.

**TA YAYA WAKILIN KOTU MAI TILASTA AIWATAR DA HUKUNCI ZAI SAN KADARORIN WANDA AKE BI BASHIN ZATA BIYA ABIN DA AKE NEMA A WAJENSA?**

Dole zaka binciko kadarorin wanda ake bi bashin, kuma ka bayar da bayanan su ga jami'in tilasta zartas da hukunci a kotu kafin ya gudanar da aikin sa.





# BAUCHI STATE JUDICIARY

## KARAMAR KOTUN BIN HAKKOKI

***LITTAFIN JAGORA***

**DAGA:**

***(Babban Magatakardan Babban Kotun Jihar Bauchi)***

SHAFI NA 1

## GABATARWA

Karamar Kotun bin hakkoki, sabon tsari ne a Nigeria
Wannan takardar jagora zata nuna muku yadda zata kasance:

→ Fara Shari'un ku
→ Shigar da Maganar bin Hakkokin kananun basussuka a Kotu
→ Samar da Kotu Mafi cancanta don bin hakkin ka
→Samarwa ko tabbatar da hukuncin da ya dace

Ansamar da wannan littafin jagora cikin harshen Hausa daga ofishin lura da Kotunan bin kananan hakkoki.

## KARIN BAYANI KAN KARAMAR KOTUN BIN HAKKOKI TA JIHAR BAUCHI

Kotun bin kananan hakkoki, an samar da ita a jihar Bauchi ranar……………………..2022, a matsayin wani reshe na kotutunan yanki da zasu samar da dama mafi sauki ga mai kara don neman hakkin sa cikin sauki akan lokaci kuma ya gamsu da tadda aka bi masa hakki ba cut aba cutarwa.
Hanyoyin bin Kadin kananan hakkoki a kotuna an samar da su ne daga dokokin kotunan lardi (na yadda ake duba alkiblar shari'un bin kananan hakkoki) na shekarar 2022.

## FA'IDOJIN KOTUN BIN KANANAN HAKKOKI

**1.** Karamar kotun bin hakkoki tana da hurumin saurarон karamar kara game bin hakki ko bashi tare da kwato hakki na hurumin da bai wuce Naira Milliyan uku ba. (N3,000,000.00).
**2.** Wannan tsari zai takaita lokaci da yawan bata lokaci don saurarон kara.
**3.** Kuma zai gaggauta tare da samar da maslaha da zata hana kai komo a tsawon kwanaki sittin (60) da za'a dauka daga lokacin da aka shigar da kara.
**4.** Za'a samu takaita daga lokacin sake saurarон kara (gaggauta ko Shirin sake saurarон kara)



## IDAN ANYI KARA A GAME DA NEMAN HAKKI KO WATA KARA TA DABAM DA KOTU TA YANKE HUKUNCI A KAINA, SHIN ZAN BIYA KUDIN DA AKA YANKE HUKUNCI A KANSA BAYAN NA SANAR DA DAUKAKA KARA.

Wannan dama ce na kotu kuma ita zata gindaya sharaddan daukaka kara.

## TA YAYA ZAN SAMU KUDIN KO HAKKINA IDAN NAYI NASARA A SHARI'AR?

Idan ka samu nasara kan karar, babu tabbacin wanda ka yi kara zai biya kudin bisa son ransa. Idan wanda kayi kara ya ki biyan kudin bisa radin kansa cikin kwanaki 14, akwai matakan doka da za a bi don tilasta shi ya biya ka jimlar hakkin ka da akayi hukunci akai.

## WANENE ZAI TILASTA A TABBATAR DA BIYAN HUKUNCI A KANSA?

Ma'aikacin zartas da hukuncin karamar kotun bin hakkoki shi zai tilasta wanzar da hukuncin.

## TA YAYA ZAN SAMU MA'AIKACI MAI TABBATAR DA ZARTAS DA HUKUNCIN A KOTU?

Za ka samu jami'in dake tilasta zartas da hukuncin karamar kotun bin hakkoki a ofishin Magatakarda.

## ME ZAN FADAWA MA'AIKACIN DON TILASTA AIWATAR DA UMARNI KO HUKUNCIN KOTU?

Za ka shaida wa ma'aikaci mai tilasta zartas da hukuncin kotu cewa kana da hakkin da kake nema a karkashin hukuncin da aka yanke. Sai ka ba jami'in tilasta zartas da hukuncin lambar shari'ar, ka shaida masa kana bukatar kotu ta aiwatar da hukuncin da aka yanke.

## KO AKWAI WANI KUDI DA ZAN BIYA MA'AIKACIN TILASTA ZARTAS DA HUKUNCI?

A'a. Jami'in tilasta zartas da hukuncin kotu ma'aikacine na babban kotun Jiha amma za ka biya kudin shirye shiryen aikin tabbatar da ganin an aiwatar da hukuncin. Ofishin Magatakardar karamar kotun bin hakkoki za su kimanta kudin da zaka biya a ofishin don dawainiyar

**BAYAN KA KAMMALA BAYANAN KA, WANDA AKE KARA ZAI BADA BA'ASI**

Wanda ake kara shima zai dauki alkawari ko ya rantse kuma ya fadi bayanan da ya sani. Kuma shima zai nuna hujjoji da dukkan shaidun sa ko takardu na shaida.

Shaidun wanda ake kara zasu iya tabbatar da shaida a madadin sa, bayan sun dauki alkawari ko rantsuwa na fadin gaskiya.

Zaka iya yiwa wanda kake kara da shaidunsa tambayoyi.

**WA ZAI YANKE HUKUNCIN SHARI'A TA?**

Kotu za ta dauki matsaya idan an gama sauraron bayanai. Kotu akasari bata daukan matsaya nan take A yawancin shari'u kotu na bukatar lokaci na dabam don yin Nazari game da karar, daga nan sai a zartas da hukunci.

**ME ZAI FARU IDAN BAN GAMSU DA HUKUNCIN KOTU BA?**

Idan baka gamsu da hukuncin kotu ba, za ka iya neman babbar kotun Jiha tayi Nazari don sake duba shari'ar ka, wannan shi ake kira da daukaka kara (Appeal)

**AKWAI ABIN DA ZAN BIYA DON DAUKAKA KARA?**

Kwarai, Hakika za ka biya kudin shirya takardun daukaka kara. Kuma za ka biya kudin samo dukkan rubutattun bayanan shari'ar domin daukaka kara a babban kotu.

**AKWAI BUKATAR NA NEMI LAUYA DON DAUKAKA KARA?**

A'a, amma idan ka dauki lauya kaine za ka biya kudin aikin tsayawar lauya kan shari'ar da kuma kudin shirya shigar da daukaka kara.

**AKWAI WATA KAYYADADDIYAR RANA DON SANARDA DAUKAKA KARA?**

Kwarai, Dole ka shigar da sanarwar daukaka kara cikin kwanaki 14 da yanke hukuncin kotu.



Mutum yana iya gabatar da karansa da kansa.

**5.** Tabbatar da bayyanar mutum da kansa a gaban kotu ( wato babu bukatar lauya domin wakiltarsa) mai kara ko wanda ake kara.

**TSARIN KARAMAR KOTUN BIN KANANAN HAKKOKI A JIHAR BAUCHI**

Karamar kotun bin kananan hakkoki a jihar Bauchi an samar dasu a wurare kamar haka: -

**1.** Babbar kotun lardi ta 7 (Chief Magistrate Court 7) Bauchi

**2.** Babbar kotun lardi ta 12 (Chief Magistrate Court 12) Bauchi

**3.** Babbar kotun majistare dake Azare (Chief Magistrate Court Azare 1) Azare

**TAKARDUN NEMAN BAYANAI (FORM)**

i. Takardar bukatar a biya
   - **SCA 1**

ii. Takardar karamar kotun bin hakkoki
   - **SCA 2**

iii. Takardar sammaci don bin hakkoki
   - **SCA 3**

iv. Takardar rantsuwar rashin isar da sammaci
   - **SCA 4**

v. Takardar neman kariya ko akasi don bin hakki
   - **SCA 5**

vi. Takardar rantsuwar isar da sammaci
   - **SCA 6**

vii. Takardar kuduri don yanke hukunci
   - **SCA 7**

viii. Takardar kudurin daukaka kara
   - **SCA 8**

**ME AKE NUFI DA KANANAN HAKKOKI?**

Karamin bin hakki shine neman hakkin da ya shafi kudi ko kwato kudin bashin da ya makale wanda bai wuce adadin naira miliyan uku ba. (N3,000,000.00)

**INA ZA KA SHIGAR DA KARAR BIN KANANAN HAKKOKI?**

Za'a iya shigar da karar kananan hakkoki a kotun da aka kebe a

Bauchi da Azare, za'a iya shigarwa a duk inda mai kara ko mai amsa kara yake da zama ko kasuwanci a jihar Bauchi
Za'a shigar da kara a wurin da wanda ake tuhuma yake zaune ko yake aiki ko yake kasuwanci a kowane yanki na jihar Bauchi.

**ME AKE NUFI DA KOTUN BIN KANANAN HAKKOKI?**
Karamar kotun bin hakkoki, ita ne kotu ta musamman inda za ka iya kara don bin hakkin kudi daga miliyan uku ko kasa da wannan adadi. Ba za ka iya yin kara don bin hakkin kudin haya ko mallakar wani abu ko jin rauni ko wahalarwa ko neman a cika alkawari a cikin alkawari a cikin karamar kotun bin hakkoki ba.
Idan neman hakkin ka ya wuce naira miliyan uku (N3,000,000.00) ba za ka iya rage kudin zuwa kasa da abin da kake neman don ya daidaita shi da naira miliyan uku ba.

**FA'IDOJIN KARAMAR KOTUN BIN HAKKOKI**
- Tana da arha da saukin mu'amala
- Bakada bukatar lauya (mai neman hakki ko mai kara)
- Kotu za ta sanar da mutumin da kake kara don neman hakkin ka

**WANENE ZAI CI MORIYAR KARAMAR KOTUN BIN HAKKOKI?**
1. Mutum wanda ya cika shekara 18 zuwa sama
2. Mutum da kasa da shekaru 18 ko wand aba shi da cikakken hankali zai iya kara a karkashin wakilin sa ko wakilin ta.
3. Kungiyoyin hadin guiwa
4. Kungiya ko Gamayya
5. Kamfanoni.

**ME YA KAMATA KAYI KAFIN SHIGAR DA KARA DON MEMAN KARAMIN HAKKI**
Sai ka rubuta takardar bukatar abiyaka hakkin ka kan takarda (Form) mai lamba SCA 1

**TA YAYA ZAN FARA YUNKURIN NEMAN HAKKI A KARAMAR KOTUN BIN HAKKOKI?**
Za a cike takardar koke ko kara da kuma bayar da takardar sammaci masu lamba (Form) SCA 2 da SCA 3



**MAI ZAI FARU IDAN NI, KO SHAIDU NA BAI IYA , KO BASU IYA MAGANA DA TURANCI BA?**
Dole ka sanar da kotu a ranar farko ta bayyanar ka a kotu cewa ba zaka iya magana ko ba ka da ilimin fahimtar harshen turanci, sai ka sanar da kotu harshen da kai da shaidunka ke iya Magana dashi.
Kotu za ta samar da wani tafinta wato mai yi maka fassara ko yi wa shaidun ka fassara idan kuna bukata.

**SHIN WANDA NAKE KARA DA NI ZA A IYA ZAMU IYA AMINCEWA MU SULHUNTA KAFIN GURFANA A GABAN KOTU?**
Kwarai, don ana bayar da karfin guiwar kowane sassan biyu su tuntubi juna da nufin daidaitawa kan lamarin a mutunce. Duk abin da ya kasance za a sanar da kotu a ranar saurararon kara game da yarjejeniyar da aka cimma kafin ranar zaman kotu, kuma kotu zata shigar da yarjejeniyar a matsayin hukuncin kotu.

**ME ZAI FARU IDAN WANI SASHE YA GAZA BAYYANA A GABAN KOTUN?**
Idan kai mai neman a bi maka hakkin ka ba ka samu bayyana a cikin kotu ba a lokacin da Magatakardan kotu ya kira karar ka, kotu zata kori karar ka.
Idan kuma wanda ake kara don neman hakki bai samu kasancewa ba a lokacin da Magatakardan kotu ya kira shari'ar, to kotu zata saurari kararka ba tare da kasancewar wanda kake kara ba. Kuma za ka iya samun nasarar shari'ar idan ka nuna wa kotu gamsasshiyar hujja ko shaidu game da karar da kayi.

**ME ZAI FARU LOKACIN ZAMAN SAURARON KARA?**
A matsayinka na mai kara, da farko zaka yi alkawari ko rantsuwar fadin gaskiya da cewar zaka fadi gaskiyar abinda ya kasance ta gefenka, kuma ka nuna wa kotu dukkan takardun bayanan ko shaidun ka. Hakkin ka ne ka tabbatar da shaida kan abinda kake nema.
Abu na gaba, Wanda kake kara zai iya yi maka Tambayoyi game da shari'ar. Idan kana da shaidu, zasu rantse sai su bada shaida. Kuma wanda kake kara zai iya yi wa shaidun ka Tambayoyi.

**ME ZAN TSARA DON FISKANTAR ZAMAN KOTU?**
Kafin zaman shari'ar ka za ka samu dukkan bayanan da za su zamo hujja kan abin da kake nema su zamo kamar haka: -

a. Rubutattun yarjejeniya ko wasika ko hotuna ko duk wata rubutacciyar shaida.
b. Takardun shaidar biyan kudi ko rasidi ko takardar chekin biyan kudi da sauran su.

**ZAN IYA AMFANI DA SHAIDU LOKACIN SHARIAR?**
Kwarai, za ka nemi shaidu lokacin shari'ar. Shaidun kuma su kasance kamar haka;

- Kai da kanka
- Ya kasance wanda yasan wani abu akan abin da kake kara a kai
- Ya kasance wanda ke da ilimi sosai ko masaniya game da abin da ka ke kara akai (wato kwararre)

**YAYA ZAI KASANCE IDAN SHAIDAN YA KI YIN SHAIDA KO YA GAZA BANI TAKARDUN DA SUKE DA ALAKA DA KARAR TAWA?**
Za ka roki karamar kotun bin hakkoki izinin tilastawa don a gabatar da shaidar ta hanyar;

Kawo takardun ko rubutattun bayanan zuwa kotu
Zuwa don tabbatar da bada shaida kan shari'ar

**WANENE ZAI ISAR DA UMARNIN KOTU ZUWA GA SHAIDAN?**
Wakili ko masinja karamar kotun bin hakkoki shine zai kai takardar umarnin kotu zuwa ga mai shaidar.

**ZAN BIYA MAI SHAIDAR DON ZUWA KOTU?**
Idan shaidan zaizo bayar da shaida a game da shari'ar ka, za ka biya kudin dawainiyar kawo shi kotu.

**AKWAI WATA KAYYADADDIYAR RANA NABADA TAKARDAR TILASTAWA SHAIDA ZUWA KOTU?**
Dole a bada takardan tilasta zuwa kotu wa shaida kafin ranar jin shari'ar.



**INA ZAN SAMU TAKARDAR SHIGAR DA KARA A KOTUN WATO FORM?**
Za ka samu dukkan takardun fara shigar da kara da tuhuma game da hakkoki kanana a ofishin magatakardan kotun a Bauchi da kotun lardi ta majistare da ke Azare da sashen bin karamin hakki na ofishin magatakardan babbar kotu a jihar Bauchi.

**WADANNE BAYANAI AKE BUKATAR NA CIKA A KAN TAKARDAR NEMAN BAHASI WATO FORMS?**

- Takardu ko hujjojinka a matsayin ka na mai kara;
- Takardu ko hujjoji game da wanda ake kara da kuma
- Bayanin abinda ake neman hakki a kansa.

Ana ba da shawara a bi dukkan ka'idojin da suke kan takardun neman bayani wato forms

**ME ZAI FARU IDAN BANI DA DUKKAN BAYANAN WANDA ZAN SHIGAR, KO SUNAN SHARI'AR?**
Za ka iya shigar da kararka ta wannan hanya.

- Yin amfani da kowane suna da aka san mutumin na aiki da shi, ko sunan kasuwanci ko sunan da mutumin ke aiki dashi a kasuwancin sa.
- Za'a sanar da kotu hakikanin sunan da zarar ka samu wani cikakken Karin bayani daga baya.

Karin Bayani: Idan baka samar da cikakken bayanin da ya dace ba zaiyi wahala ka samu abin da kake nema ko da kayi nasara a shari'ar.

**YAYA ZANYI DA TAKARDUN DA NA CIKE WATO FORMS:**
Za a mika takardun da aka cike zuwa ga magatakarda ko wanda ke da hakkin lura da ofishin magatakardan kotun lardi ta majistare da aka shigar da koken ko karar.

**KO ZAN BIYA WANI ABU DON SHIGAR DA KARAR NEMAN HAKKI?**
Kwarai, dole ka biya kudin kotu don bin diddigin neman kananan hakkoki a ofishin magatakarda.

**SHIN WANDANAKE KARA ZAI IYA KARA TA?**

Kwarai, Wanda kake kara shima zai iya shigar da kara makamanciya a kan ka. A karamar kotun bin hakkoki, makamanciyar shigar da kara ba za ta wuce adadin kudi naira miliyan uku ba. (N3,000,000) amma banda kudin ruwa ko kudin dawainiya, wanda ake kara zai iya amincewa da wani sashe ko dukkan kara kuma duk za a shigar a cikin abin da ake nema a wajensa ko wajenta.

**TA YAYA ZAN SANI IDAN WANDA NAKE KARA SHIMA YA SHIGAR DA KARA MAKAMANCIYAR TAWA?**

Wanda ake kara idan ya yi niyyar sake shigar da kara kan abinda shima yake nema dole zai kasance ya yi hakan ne cikin kwanaki bakwai, daga ranar da aka bashi sammaci. Kuma kaima za a baka takardar neman hakki ta hannun wakili ko ma'aikacin kotu.

**IDAN WANDA NAKE NEMAN HAKKI WAJEN SA SHIMA YA YI KARATA, SHIN ZA A IYA DAGA LOKACIN ZAMA?**

Idan ka samu sanarwar korafi a kan neman hakki da kake yi kafin ranar yanke hukunci, dole ka shirya hujjojin ka kuma ka gabatar da su don kare kan ka game da korafi da ake yi maka kafin ranar yanke hukunci. Kuma ba za a daga kara ba saboda wanda ka ke kara shima ya yi karar ka, sai ko idan ba a sanar da kai cewa wanda ka ke kara shima ya shigar da kara makamanciya a kan ka ba tun kafin ranar sake zaman kotu.

**WANENE ZAI SANAR DA WANDA NAKE KARA KAN BIN HAKKINA?**

Wakili ko masinjan karamar kotun bin hakkoki zai isar da sammaci zuwa ga wanda ake kara hannu da hannu. Idan wanda ake kara bai samu sammaci a hannun sa ba, wakilin kotu zai cike takardar gaza isar da sammacin, ko kuma Magatakarda ko wakilin Magatakardan karamar kotun bin hakkoki zai sanar da kai bukatar sake wata hanyar ko tsarin kai wani sakon sanarwa ko sammacin.

**WADANNE BAYANAI SAMMACIN ZAI KUNSA DON ISARWA GA WANDA AKE KARA?**

Sammacin zai samar da wanda ake kara;



- A kan wane abu ake karar sa
- Nawa ne adadin kudin da kake nema a wajen sa
- Ranar zaman kotun bin bahasin kananan hakkoki

Ba za ka samu zaman kotu ba idan wanda ake kara bai samu sakon sanarwar wadannan bayanai ba.

**WANE ABU ZANYI A RANAR SAURARON KARA?**

- Ka halarci kotu da wuri
- Ka nemi harabar ofishin da kotun zata zauna.
- Ka tambayi Magatakardan kotu idan shari'ar ka tana cikin wanda za a saurara a ranar.

**TA YAYA ZAN SAN WANE LOKACI ZA A FARA SAURARON SHARI'A TA?**

- Magatakardan kotu zai kira karar ka da sunan ka
- Sai ka tashi tsaye ka amsa sunan ka
- Idan kai da wanda kake kara kuna halarce kuma kun shirya sai a fara sauraron shari'a.

**ZAN IYA DAGA KARAR DA NAKE YI?**

A matsayin wanda kake kara za ka iya rokon kotu ta daga sauraron karar saboda wani muhimmin dalili, amma sau daya a tsawon lokacin shari'ar. Idan kuma kai ake kara za ka iya neman kotu ta daga sauraron karar saboda wani muhimmin dalili amma sau daya a tsawon lokacin sauraron karar.

**TA YAYA ZAN BUKACI KOTU TA DAGA LOKACIN SAURARON KARATA?**

Ta hanyar aika wasika zuwa kotu da kuma daya gefen don neman kotu ta daga ranar sauraron karar kafin ranar yanke hukunci. Kotu za ta saurari takardar ka ta neman daga lokaci amma sau daya tak saboda wasu dalilai na musamman.

Idan kai ko wakilinka ba zai iya zuwa kotu a ranar shari'ar ba , kotu za ta karanta takardar ka, amma bai zamo wajibi ta daga sauraro bai dan bata gamsu da dalilan da ka bayyana a cikin wasikar ka ba kuma za a iya korar shari'ar ka.

Idan kai ake kara kumaba ka iya samun bayyana ba lokacin zaman kotu, hakika kotu zata iya yanke hukunci a kan ka ko bakanan.